رمضان دعوة الى ضيفة الله

الشيخ حسن الصفار

# WATAN RAMADHAN-GAYYATA ZUWA GA LIYAFAR ALLAH.

MARUBUCI: SHAIKH HASAN SAFFAR

MAI FASSARA: DAYA DAGA LAJANAR TARJAMA-BAUCHI NIGERIA

## GABATARWA

Watan Ramadhana kwazarin falala ne da albarkatu da alqalami ya gaza wajen bayyano sirrinsu ko bayyana iyakar tasirin shi watan a rayuwar mutum musulmi.

Akwai nassosi da dama da suka zo game da falalarsa kamar kuma yadda marubuta da mawallafa masu yawa suka yi rubuce –rubuce game da shi wannan wata mai alfarma.

Ya wadatar game da falalarsa cewa an danganta shi ga Allah da kiran sa cewa shi watan Allah ne ba sauran watannin ba duk kuwa da cewa sauran watannin ma Allah ne Ya halitta su.

To tambaya a nan ita ce, mene ne ya sa aka kebanci wannan wata aka danganta shi ga Allah? Ashe wannan ba wata ishara ce ba da ke nuna cewa akwai wata ’yar mararrabiy ta musamman wadda wannan watan ya kebanta da ita? Shin wannan wata na Ramadhana mene ne ma’anarsa?

## FALALAR WATAN RAMADHAN

Domin sanin falalar wannan wata da kuma fahimtar don me Allah Ya kebance shi Ya zabe shi ba sauran watanni ba, za mu yi dubi ga wasu jawabai daga Manzon Allah (S).

Manzon Allah (S) ya ce:-

قال الرسول(صلى الله و اله و سلم)

" انماسمي الرمضان لأ نه ير مض الذنوب "

(177\2ج الحكمة ميزان)

"An sanya masa suna Ramadhana ne saboda yana qone zunubai". (Mizanil Hikma Juzu'i na 4 shafi na 177).

Ya zo daga gare shi (S) yayin da watan Ramadhana ya kusato ya ce,

"Subhanallah, me kuke fuskanta, mene ne ya fuskanto ku? Ya fada har sau uku…

A bisa dukkan alamu a kowace shekara idan watan Ramadhan ya kusato, a qarshen watan Sha'aban yakan yi huduba domin ya farkar da zukatan al'umma game da kusatowar watan Allah.

Akwai ruwayoyi da dama da bayanai dabam-daban game da haka; daga cikinsu akwai wadanda aka ruwaito daga Imam Ridha (A.S.) daga iyayensa da kakanninsa daga Amirul Muminina, Ali bin Abi Talib (A.S.) ya ce:-

"Haqiqa wata rana Manzon Allah(S) ya

yi mana huduba inda ya ce:-

"أيها الناس انه قد أقبل اليكم شهر الله بالبركة والرحمة و المغفرة"

"Ya ku mutane haqiqa watan Allah ya zo muku da albarka , da rahama, da gafara,watan da a gurin Allah shi ne mafificin watanni,ranakunsa su ne mafifitan ranaku,dararensa su ne mafifitan darare, awoyinsa su ne mafifitan awoyi, watan da a cikinsa aka gayyace ku zuwa ga liyafar Allah kuma aka sanya ku a cikin ma'abuta karamar Allah,numfashinku a cikinsa tasbihi ne ,barcinku a cikinsa ibada ne, ayyukanku a cikinsa karbabbu ne, addu'arku a cikinsa amsasshiya ce, saboda haka ku roqi Allah Ubangijinku a cikinsa da niyya ta gaskiya,da zukata tsarkakakku, Ya ba ku dacewar yin azuminsa,da karanta littafinSa, domin (matsiyacin) mutum mafi hasara shi ne wanda aka haramta masa gafarar Allah a wannan watan mai girma.

Yunwarsa da qishirwarsa su tuna muku yunwa da qishirwar Ranar Qiyama, ku yi sadaka ga faqiranku da miskinanku, ku rumtse idandunanku daga ganin abinda ganinsa bai halatta ba, ku hana kunnuwanku jin abinda bai halatta a saurare shi

ba,ku tausasa ga marayu za a tausasawa marayunku,ku tuba gare Shi daga zunubbanku,ku daga hannuwanku gare Shi a lokacin yin addu'a a lokutan sallolinku domin haqiqa wadannan lokatan su ne mafifitan awoyi da Allah Mai girma da daukaka Yake duba na rahama ga bayinSa Ya amsa musu idan sun roqe Shi.

Ya ku mutane rayukanku garkuwa ne ga ayyukanku saboda haka ku fanso su ta hanyar istigfari, bayanku kuma ya nauyaya da abubuwan da kuka labta masa saboda haka to ku rage musu nauyin ta hanyar doguwar sujadarku, ku sani cewa Allah Madaukakin Sarki Ya yi rantsuwa da IzzarSa cewa ba zai azabtar da masu salla masu sujada ba, kuma ba zai firgita su da wuta ba ranar da mutane ke tsayuwa ga Ubangiji.

Ya ku mutane wanda ya ba da buda baki ga mai azumi mumini a cikin wannan watan to yana da ladan wanda ya 'yanta wuyaye da kuma yafiyar abinda ya gabata na zunubansa.

Daga nan sai aka ce masa, "Ya Manzon Allah ai ba dukkanmu ne za mu iya yin haka ba. Sai ya ce: "To ku kare kanku daga wuta koda kuwa da gwargwadon tsagin dabino ne, ku kare kanku daga wuta koda kuwa da shayar da maqwarwar ruwa ne,

domin Allah Ta'ala zai bayar da wannan ladan ga duk wanda ya aikata gwargwadon dan qalilan idan ba zai iya yin fiye da haka ba.

Ya ku mutane wanda ya qara kyautata dabi'unsa a wannan watan to zai qetare siradi ranar da qafofi suke zaamewa a cikinsa,wanda ya yi rangwame ga baiwarsa a wannan watan Allah zai masa rangwame a hisabinsa,wanda ya kame sharrinsa Allah zai kame fushinSa daga gare shi ranar da zai gamu da Shi,wanda ya girmama maraya a cikinsa Allah zai girmama shi Ranar da zai gamu da Shi,wanda ya sadar da zumunta a cikinsa to Allah zai sadar da shi da rahamarSa ranar da zai gamu da Shi,duk kuma wanda ya yanke zumuntar a cikinsa to Allah zai yanke shi daga rahamarSa ranar gamuwarsa da Shi. Wanda ya yi sallar nafila a cikinsa Allah zai rubuta masa 'yantuwa daga wuta ranar Qiyama.Wanda ya aikata farilla kuwa a cikinsa to yana da ladan wanda ya aikata farilla saba'in na wasu kwanaki na

watannin da ba wannan watan ba, wanda ya yawaita yin salati gare ni to Allah zai nauyaya masa ma'auninsa ranar da ma'auni yake zamantowa marar nauyi, wanda ya karanta aya guda daya ta Alqura'ani to yana da ladan wanda ya sauke Alqura'ani a kwanaki na sauran watannin.

Ya ku mutane qofofin Aljanna an bubbude su a wannan watan ku roqi Ubangijinku kada Ya kulle su gare ku, qofofin wuta kuma a kukkule suke ku roqi Ubangijinku kada Ya bude su gare ku, Shedanu kuma a daddaure suke ku roqi Ubangijinku kada Ya sake su a kanku." (Littafin Mafatihul Jinan)

To da yake muna kusantowa ga watan Ramadhana mai alfarma ne ya kamata mu yi godiya ga Allah da yabo gare Shi da Ya yi ni'ima gare mu Ya kawo mu zuwa ga wannan wata domin mu zamanto masu shiga cikin liyafar wannan wata mai girma, domin akwai mutane da yawa wadanda suka riga suka cika ajalinsu tsakanin wancan Ramadhan din da ya wuce da kuma wannan da ya iso.

Mutum nawa ne wadanda rayukansu ke cikin barazanar halaka ta fuskar mutuwa irin wadda aka saba da kuma wadda ke aukuwa farat daya ta hanyar hatsarin abin hawa.

Muna roqon Ka Ya Allah Madaukaki Ka ba mu dacewar yin azumi a wannan watan, Ka karbe shi daga gare mu ,   kuma Ka amintar da mu a cikinsa, Ya zamanto yayin da wannan watan yake kawowa qarshe Ka yi mana afuwa Ka gafarta mana ,Ka yi mana rahama.Domin  Kai ne mafi Rahamar Masu rahama.

FASALI NA DAYA

كيف نستثمر رمضان؟

YAYA ZA MU FA'IDANTU DAGA WATAN RAMADHANA?

Tambayar da ke maimaita kanta a zuciyar kowane mumini ,ita ce ta yaya za mu fa'idantu da watan Ramadhana,domin bai wadatar ba mutum kawai ya rayu a cikin wannan wata ba tare da kaiwa ga manufarsa ba,babu makawa mutum ya yi qoqarin kaiwa ga manufarsa.

Haqiqa watan Ramadhana tamkar ruwan sama ne da ke kwararowa a kan qasa, akwai qasa jigawa mai kyau ,akwai kuma wata qasar qequwa ce, kowacce tana karbar ruwan sama ta tafi tare da shi gwargwadon irinta da kuma irin yanayinta,wata za ta fito da tsirrai wata kuma ruwan ba ya qara mata kome illa chakudewa da mandaqewa;su mutane ma tamkar haka suke wajen amfana da watan Ramadhana.Wasu mutane zukatansu kan amfana daga wannan watan mai alfarma su kai ga samun sa'ada da alheri,wasu kuma wannan wata yakan shude musu ne tamkar shudewar gajimarai, sai dai ma ya qara musu hasara da tsiyacewa kamar dai yadda ya zo a hadisi daga Manzon Allah(S) cewa:

"الشقي من حرم غفران الله في هذ الشهر الكريم"

“Mafi tsiyacewar mutane shi ne wanda aka haramta masa gafarar Allah a wannan watan” ( Mizanul Hikma juzu'i na 4 shafi na 180).

Idan har ana son zuciyar mutum ta canza ta zamanto lambu da qamshin furannnin taqawa da aikin qwarai ke busowa daga gare shi to babu makawa a tsara wani jadawali na aiki a wannan watan domin ya zamanto kadarkon ruhi mai bubbugar da Imani.

Sai dai kuma shin akwai wani jadawi ko tsari ne da ya fi tsarin Ma'asumai musamman ma Amirul Muminina Ali bin abi Talib (A.S.)? Domin akwai wata fitacciyar wasiyyarsa wadda zai yi kyau idan da kowane daya daga cikinmu zai dauke ta a matsayin tsarinsa na aiki a watan Ramadhana.

Ita dai wannan wasiyya tana da siffofi guda biyu da suka sanya ta ta sha bambam wadanda su ne :-

Wannan wasiyya ya yi ta ne a cikin watan Ramadhana, wanda ke nuni da cewa wannan ta zo daidai da lokacin da ake bukatar tafiya tare da watan Ramadhana.

Ita ce kalma ta qarshe da shi Imam Ali (A.S.) din ya yi domin fahintar da mutane, wadda kuma abu ne sananne cewa Kalmar manyan mutane ta qarshe takan qumshi qwarewarsu ta rayuwa da darrusa da suke so su qaddamar wa zuriya da al'umma masu zuwa.

Imam Ali (A.S.) na daga cikin manyan mutane magabata a tarihi bayan Manzon Allah(S).

Da yawa daga cikin manyan mutane a tarihi sukan zamanto sun shahara ta wani bangare ko fanni guda ayyananne, misali kamar ta fannin ilimi kawai,ko ta fannin soja kawai, ko ta fannin adabi kawai,ko ta fannin ilimin zamantakewa kawai amma Imam Ali (A.S.) ya shahara ta kowane fanni da kowace fuska,rayuwarsa cike take da darrusa da qwarewa da ya kwankwada daga Manzon Allah(S) da qwarewar a gogayyar da ya yi wajen arangama da magabta masu qiyayya ga addini.

La'alla wasiyyarsa ta qarshen rayuwarsa na koyar da al'umma taqaitacciyar qwarewarsa a rayuwa da kuma ba mu abu mafi muhimmanci da yake gani lalle muna da bukatarsa a rayuwa.

Muna ba da shawarar cewa wannan wasiyya ta zamanto tsarin manhaja ko tsarin jadawalin aikinmu a watan Ramadhana, kowane mumini ya karance ta ya haddace ta.

Sananne ne cewa haddace nassosi da hadisai na da falala mai yawan gaske. Ya zo daga Annabi Muhammadu(S) cewa:-

"Wanda ya haddace hadisi arba'in daga al'ummata yana neman yardar Allah da haka da kuma sakamakon Lahira to Allah zai tayar shi tare da Annabawa da Siddiqai da Shahidai da Salihai to wadannan kuwa su ne wadanda yin abuta da su ya kyautatu".

(Mizanil Hikma Juzu'i na 2/29 )

"Wanda ya haddace hadisai arba'in daga al'ummata a kan halal da haram Allah zai tayar da shi a Malami Ranar Alqiyama kuma ba zai azabtar da shi ba".

Saboda haka ya kamata mutum ya haddace abinda zai iya daga ayoyi da hadisai masu daraja.

Wasu daga cikinmu suna taqaitawa da gamsuwa da riqe ra'ayoyi da ma'anoni da aka ciro daga nassosi kawai ba tare da sun haddace su nassosin ba. Yin haka kuwa

na sanya mutum ya haramta wa kansa fa'idoji masu yawa, domin haddace ayoyin Alqura'ani da kalmomin Ma'asumai na haskaka zuciyar mutum tare da ba shi kwanciyar hankali da koyar da shi tsayuwar daka yayin tsanani da da jarrabawa.

'Yan'uwa da ake kamewa ana aika su gidan yari da masu shiga cikin mawuyacin hali sun san gaskiyar wannan al'amarin sarai!

A nan mun yi tanbihi ga 'yan'uwa cewa azumi na daya daga abubuwan da ke qarfafa hadda, ya zo a hadisi daga Manzon Allah (S) cewa :-

"Abubuwa uku suna gusar da mantuwa kuma suna kaifafa qwaqwalwa: Karatun Alqura'ani da yin aswaki da yin azumi". (Mizanul Hikma Juzu'i na 2 shafi na 453)

وصيةالأمام علي (عليه السلام)للحسن والحسين لما ضربه ابن ملجم لعنه الله

WASIYYAR IMAM ALI (A.S.) GA IMAM HASAN (A.S.) DA HUSAIN (A.S.) YAYIN DA BIN MULJAM LA'ANANNEN ALLAH YA SARE SHI.

"أوصيكمابتقوى الله وأن لا تبغي الدنيا و ان بغتكما"

"Ina yi muku wasiyya ku ji tsoron Allah da kuma cewa kada ku nemi duniya ko kuwa ita ta neme ku, kuma kada ku yi baqin ciki game da wani abu nata da aka kange shi daga gare ku, ku fadi gaskiya ,ku yi aiki don samun lada, ku zamanto masu artabu da azzalumai masu taimakawa ga wanda ake zalunta".

"Ina yi muku wasiyya ku biyun nan da dukkanin 'ya'yana da iyalaina da duk wanda rubutuna ya isa gare shi da ku zamanto masu tsoron Allah masu tsari a al'amuranku da sulhunta tsakaninku, domin ni na ji kakanku yana cewa: sasanta tsakani ya fi dukkan salla da azumi".

"Ku tuna Allah! Ku tuna Allah game da Marayu kada cutar da bakunnansu. Kada a tozartar da haqqoqinsu a gurinku".

"Ku tuna Allah ku tuna Allah game da maqwabtanku domin su wasiyyar Annabinku ne, bai gushe ba yana nanata wasici game da su har sai da muka yi tsammanin zai sanya su masu cin gado ne".

"Ku tuna Allah ku tuna Allah game da Alqura'ani kada wani ya riga ku aiki da shi ba ku ba".

"Ku tuna Allah, ku tuna Allah game da salla domin ita jigon addininku ce."

"Ku tuna Allah ku tuna Allah game da Dakin Ubangijinku kada ku yi watsi da shi ya zama wayam matuqar kuna raye domin idan kuka yi watsi da shi to ba za ku ga juna ba".

"Ku tuna Allah ku tuna Allah game da Jihadi da dukiyarku, da rayukanku da harsunanku , a tafarkin Allah".

"Ku zamanto masu sadarwa masu bayarwa, ku kiyayi juyawa da yankewa"

"Kada ku dena yin umarni da kyakkyawa da hani da mummuna don kada Ya dora ashararanku a kanku sa'an ku yi addu'a kuna roqon Sa Ya qi amsa muku".

"Ya ku Banu Abdulmuttalib ban lamunce muku zubar da jini malala ba kuna masu cewa ai an kashe Amirul Muminina ne ".

"Kada ku kashe kowa sai wanda ya kashe ni kawai, ku dakata idan har na mutu a sakamakon wannan saran nasa to sai ku yi masa sara daya gwargwadon sara, kuma kada ku yi gunduwa- gunduwa da shi mutumin,domin haqiqa na ji Manzon Allah(S) yana cewa: "Ku kiyayi gutsuttura gawa koda ta mahaukacin kare ce".

(NAHJUL BALAGHA)

من هدي الوصية

SHIRYARWA DAGA WASIYYAR

Wannan wasiyya ta tattara ne a kan cibiya guda kuma ta shafi bangarori dabam-daban na rayuwar dan Adam. Saboda haka ya dace mu haddace mu yi nazarin wasu muhimman bangarorinta game da rayuwa.

Na farko Taqawar Allah:

Taqawa ko kuma tsoron Allah wasiyya ce ta dukkan Annabawa da Manzanni da Imamai kafin su kuma wasiyyar Allah ce ga dukkan bil Adama baki daya da dukkan zuriyoyi masu zuwa, Allah Ta'ala Yana cewa:-

ولله ما في السموت و ما في الأرض و لقد وصينا الذين أوتواالكتب من قبلكم واياكم أ ن اتقوا الله و ان تكفروافان لله ما في السموات و ما في الأرض و كان الله غنيا حميدا

(النساء:131)

"Haqiqa Mun yi wasiyya ga wadanda aka ba wa littafi kafin ku da ku kanku cewa ku ji tsoron Allah, idan kuwa kuka kafirce to duk abinda ke cikin sammai da qasa na Allah ne, kuma Allah Ya kasance Mawadaci ne Abin godewa."

An tambayi Imam Sadiq (A.S.) tafsirin ma'anar taqawa inda ya ce:-

سأل الأ مام(عليه السلام) عن تفسير التقوى فقا ل:

"أن لا يفقدك حيث أمرك و لا يراك حيث

نهاك"

(ميزان الحكمة ج10 \636)

"Shi ne Kada( Allah )Ya rasa ka a gurin da Ya umarce ka, kuma kada Ya iske ka a gurin da Ya hane ka."(Miazanul Hikma Juzu'i na 10 shafi na 637).

A wani qawlin kuma taqawa na nufin aiki da koyarwar addini. Imam Ali (A.S.) ya ce:-

"Mai taqawa shi ne wanda ya kiyayi aikata zunubi"

"Kan taqwa shi ne barin sha'auce-sha'auce"

"Duk wanda ya mallaki sha'awarsa to ya zama mai taqawa."

Abu ne sananne cewa mutum yana da sha'auce-sha'auce da kwadayi iri dabam-daban, kamar sha'awar jinsi, da sha'awar shaqatawa,amma duk mutumin da ya danne sha'awarsa ya kame kansa to zai zamanto mai taqawa.

Azumin wajibi wanda watan Ramahana ya kebantu da shi manufarsa ita ce dasa taqawa a zuciyar mutum da qarfafa ta a kan kansa. Allah Ta’ala Yana cewa:-

"يا يها الذين أمنوا كتب عليكم الصيام كما كتب على الذين من قبلكم لعلكم تتقون"

(البقرة:183)

“Ya ku mutane haqiqa an farlanta muku azumi kamar yadda aka farlanta a kan wadanda suka gabata kafin ku ko kwa samu ku zama masu taqawa”. (Surar Baqara aya ta 246)

A halin yanzu ba wai muna nufin mu yi bayani game da taqawa da darajojinta ba ne illa iyaka dai muna nufin mu ba da amsa ne game da tambaya mafi muhimmanci wadda ita ce ta yaya mutum zai zamanto mai taqawa?

**Ta Yaya Mutum Zai Zamanto Mai Taqawa?**

Kowane mumini yana fatan kaiwa ga darajar taqawa amma tambaya ita ce, wadanna abubuwa ne suke kai mutum zuwa ga taqawa?

Fahimta

Mafi yawancin mutane da suke fandarewa, ba sa riqo da umarnin Allah dalilin da ke kai su ga haka shi ne jahilci game da koyarwar addini da rashin fahimtar sa; ya zo daga Manzon Allah (S.A.)

“Dukkanin taqawa ita ce ka koyi abinda ka jahilta kuma ka yi aiki da abinda ka sani”. (Mizanul Hikamah Juzu’ii na 10 shafi na 646)

Sananne abu ne cewa fahimta ko fadaka na daga cikin abubuwan da ke taimakawa ga mutum ya kai ga darajar taqawa.

“Kowane abu yana da sinadari, sinadarin taqawa shi ne zukatan masana”.

Saboda haka ya kamata mutum ya zauna da ma’abuta tuntuntuni daga cikin malaman musulunci ya kuma ziyarci littattafa musulunci domin nazarin rayuwar Manzon Allah (S) da zuriyar gidansa domin ya samu sani, har ila yau ya zamanto mai sauraron hudubobin malaman addinin musulunci domin qara samun fahimta.

Tsarin Gyara Zuciya

Idan mutum yana so ya kai ga darajar taqawa to lalle ne ya kewaye kansa da tsari mafi kyau na gyara zuciya; kamar yin karatun Alqura'ani, da karanta addu'o'i da sallar qiyamul layli da sallolin nafila da kuma azumin tadawwu'i

Yanayi Mai dacewa

Idan mutum ya rayu a guri lafiyayye to zai sami qarfin gwiwar zamantowa mai taqawa mai aikata aikin qwarai yadda galabi wannan yakan kai mutum ga taqawa.

و نظم أمركم

NA BIYU: Tsara Al'amuranku

Saboda wagegen fagen Musulunci da ya game duniyarmu ta qasashen musulmai akwai mutane da dama da suka yunquro daga cikin wannan al'umma tamu suna qoqarin aiki a tafarkin Allah don kawo gyara da yin hidima ga addini sabanin marhalar da ta gabata yadda masu qoqarin kawo gyaran suka kasance, 'yan qalilan ne alhali mafiya yawa su gafalallu da suka kasance suna rayuwar 'yan baruwanmu game da al'amuransu.

Babu shakka cewa a yau al'umma ta kama tafarkin shiriya da farkawa ,ana qoqartawa wajen ayyukan taimakon musulunci,har ma ta bangaren wasu da a zahirinsu ba su damu da riqon addini ba amma yanzu idan ka fara tattaunawar addini da kuma halin da al'umma take ciki sai ka ga suna ba da bayani yadda ya dace kuma mai kyau mai ma'ana.

Amma inda mushkila take shi ne a gurin aikin 'yan daidaiku da kuma na gamayya wajen yunqurawa a aikace inda za ka iske abin yana tafiya ba yadda ake so ba ,abu da ake bukata shi ne a hade qarfi guri guda kowa da kowa don fuskantar abu guda.

Imam (A.S.) yana yi mana wasiyya da mu tsara al'amuranmu domin yin hakan yana da muhimmanci matuqa.

Abinda ake nufi da tsara al‘amuranmu shi ne hado qoqarinmu da qwarewarmu dabam-daban daga mutane da gurare mabambanta zuwa guri daya mu zamanto qarfi daya domin yin aiki ga al‘umma.

Dangane da wannan nahiyarmu ta riga ta yi wasu matakai zuwa gaba, domin wasu cikin qungiyoyin taimakon al‘umma suna taimaka wa gajiyayyu da faqirai. A halin yanzu akwai tsari da darrusa ingantattu alhali a da can babu irrinsu na koyar yadda za a tsara sadaka da kyautuka da taimakon agaji.Wannan irin tsarin shi kansa alama ce kuma shaidar tsara al‘amuranku da Imam ya fada.

Aikin wayar da kan jama‘a shi ma yana bukatar a yi masa tsari mai kyau, saboda haka akwai bukatar ma‘abuta huduba da Malamai da marubuta da gwanayen masu waqe su zaman suna da hadin qarfi guri guda da aiki bai daya wajen fahimtar da jama‘a halin da al‘aumma ke ciki ba tare da aiki a rarrabe ba da zai iya kai ga rarrabar jama‘a ba.

Alal misali a watan Ramadhana lokaci ne mai girma da ya dace mai huduba ya hau kan mumbari don fahimtar da mutane da fadakar da su.Amma tambaya a nan ita ce ta yaya mai hudubar zai yi kuma game da me zai fahintar da mutane.

Shin akwai wani hali ne ko yanayi na siyasa da mai huduba babu makawa ya yi bayani game da shi a wannan watan? Shin wace hanyar fahimtarwa ce mafi dacewa wajen fahintar da jama‘a?

Amsa wadannan tambayoyi na lizimtar cewa masu hudubobi su hadu a duk inda suke, a kowani gari ko a birni ko a qauye,su zauna tare domin su cim ma matsaya guda domin su tsara abinda za su yi ya zamanto daya.

Ina ma da za a sami wasu muminai su amsa irin wannan ganawar a qarqashin kowane suna ko sunaye ne da suke bukata .

Haka nan ma ya kamata a sami wata tattaunawar dangane da halin da malamai suke ciki, don me suka sami sabani da rarraba hatta a kan al‘amura masu sauqi kamar su tabbatar da kamawar watan Azumi da watan qaramar salla?

Ko shakka babu mafi girman dalilin aukuwar haka shi ne rashin haduwarsu da juna da tattaunawa da juna dangane da al‘amuransu da mushkilolinsu.

Imam Ali (A.S.) ya ce:-

“ Haqqi ne ga mai hankali ya qara ra‘ayin masu hankali a kan ra‘ayinsa kuma ya qara ilimin masu hikima a kan iliminsa.

‘‘Wanda ya karbi fuskokin ra‘ayoyi da yawa to zai san guraren kuskure dabam-daban‘‘

Mai yiwuwa akwai dalilai biyu da ke hana malamai aiki a matsayin jama‘a guda:-

Tsoron yadda hukuma za ta yi martani ga al‘amarin ,domin wadansu daga cikin Malaman na da imanin cewa za a iya yi musu kallon jama‘ar ’yan siyasa kuma hakan zai kai ga daukar mataki na hamayya da qiyayya har a kai ga murqushe su.

Amma tambaya ita ce har zuwa yaushe za a yi ta jin tsoron fushin hukuma,da qoqarin yardar da ita tare da jingine koyarmu ta addininmu da ladubbanmu?

Idan da iyaye sun kasance suna da irin wannan ra‘ayin ko tunanin to da ba su bar ’ya’yansu suna halartar koda taron zaman makokin Husainiyya ba.’’

Wannan al‘amari babu abinda yake bukata illa tsayuwar daka da jarumtaka.Bilhasali ma ai irin wannan taron ba shi da wata alama da ke nuna cewa taro ne na siyasa, sai dai kawai nashadi ne da taron ilmantarwa kawai ga al‘umma ta yadda koyar da mutane game da dabi‘un qwarai da aqida da ruhi da ake bukata a wannan zamani.

Shamakin zuciya

Akwai wani irin shamaki a zukatan da yawa daga cikin masu huduba da kuma malamai wanda sau da yawa yakan hana da dama daga cikinsu yin aiki da gamayyar jama‘a sai dai a daidaiku dalili kuwa shi ne aikin ’yan daidaiku shi ne ya fi sauki fiye da na yi a cikin jama‘a.Amma kuma alal haqiqan aikin canja al‘umma ya fi yiwuwa da ba da sakamako da samar da tasiri sosai ta hanyar gamayya da yin aiki hanyar qungiya tsararriya.

Juyin Musuluncin da ya bulluqo a Jamhuriyar Musulunci ta Iran ba ya bullo ne kawai rana a tsaka ba har aka kai ga cin nasara, abu ne da yake sakamakon aikin qungiyoyin da malaman addini suka assasa kuma suka shugabanta shekara da shekaru, kamar su „"Qungiyar Malaman Addini 'Yan Gwagwarmaya, da "Jam'iyar Hadin Kan Qungiyoyi tare kuma da sauran wadanda suka samar da Jam'iyyu na siyasa da Mu'assasan Taimakon Jama'a iri dabam-daban, da Mu'assasar Taimakon Shahidai da Raunanan Mutane.

Saboda haka alal haqiqa idan har al'ummarmu na buqatar canji ba zai yiwu ba tare da hadin kai ba, masu yaqar ayyukan mu'assasu su ma don suna da mummunar fahimta ne game da mu'assasa, alhali kuwa idan aka tsara al'amuran ayyuka sukan zamanto an yi su cikin sauqi. Aikin mu'assasa ba wani abu ne fiye da hada qarfi da qarfe guri daya ba,sai sanya mata suna ayyanane da gudanar da ayyukan a bisa tsarin da aka gamsu da shi ;sunan mu'assasa ba shi ne mafi muhimmanci ba,abu mafi muhimmanci shi ne ayyukan da take yi da kuma abinda ta qunsa.

Kamar yadda muke bukatar tsari a aikin alheri haka nan a ayyukan siyasa domin gudanar da ayyukan siyasa ba zai yiwu ba ba tare da tsari ba. Lalle ne mutane su fahimci cewa matuqar suna bukatar kawo canji a tsarin da ake da shi to lalle ne a kawo tsari na siyasa. Dukkanin irin wadannan mu'assasai da cibiyoyi duk sun shiga cikin ma'anar tsara al'amuranku da Amirul Muminina yake nufi.

Na Uku: Sasanta Tsakaninku:-

صلاح ذات بينكم :-

"و صلاح ذات بينكم فاني سمعت جدكما (صلى الله عليه و اله) يقول من أصلح ذات البين فانها أفضل من عامة الصلاة و الصيام".

"Da sasanta abinda ke tsakaninku domin na ji kakanku, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da zuriyarsa yana cewa:sasanta abinda ke tsakanin ya fi salloli baki daya da azumi baki daya."

A wannan zamani al'ummarmu na da bukatar wannan wasiyya a sakamakon abinda ake da shi na sabani da hamayya da rarraba.

Wannan mushkila da sabani suna aukuwa ne a sakamakon jahilci da kuma ingiza mai kantun ruwan hukuma game da haka, zugar hakuma kuwa abu ne sananne domin dagutai na kowane zamani haka suka kasance suna yi a duk tsawon tarihi. Duk yayin da suka ga wata jama'a suna qoqari ta wata fuska da ta saba wa al'amuransu sai su yi amfani da dabarar nan da ake ce rarraba su ka mulke su a wajen dakatar da wannan yunqurin ko daqushe shi.

A halin yanzu ta riga ta faru ta qare hatta a tsakanin malaman addini,da masu huduba a kan mumbari,mutum sai ya hau kan mumbarin makokin Imam Husain(A.S.) ya yi amfani bugun qirjin shahadar Imam Husain(A.S.) ya yi suka a sarari ko a fakaice ga masu yi wa musulunci hidima har ya iya komawa gida ya yi barcinsa ya qoshi, alhali kuwa ma'abuta gwagwarmaya da qoqarin kawo gyara suna can suna gudun hijira a wajen qasa ko suna maqare a gidajen kurkuku suna shan azaba da gallazawa iri-iri.

A halin yanzu da hukuma ta ji hatsarin yunqurin jama'a na nuna rashin gamsuwa da ita sai ta ga cewa babu hanya mafi dacewa da za ta yi amfani da ita sai hanyar cusa sabani da fada da juna a tsakanin al'umma;musamman ma da suka ga yunqurin juyin juya hali yana qaruwa saboda haka suke qoqarin daqushe wannan yunqurin ta hanyar yada ji-ta ji-ta da tuhumce-tuhumce da yada qiyayyar masu addini.Bugu da qari kuma suna haduwa da gaulayen mutane masu mugun shiri har al'umma ta rabu kashi biyu ; masu goyon bayan malaman addini da masu qin goyon bayan malaman addini.

Abin al'ajabi da ban takaici kuma shi ne masu sasanta tsakani sun yi qaranci,su 'yan qalilan din ma aikinsu yakan taqaita ne a kan al'amuran daidaiku kamar sasanta tsakanin ma'aurata-miji da mata in sun sami sabani a shiga a sulhunta su,wannan shi ma abu ne mai kyau amma akwai wanda ya fi muhimmanci wanda ya qunshi sasantawa tsakanin qasa da qasa, ko tsakanin qungiya da qungiya!

Ina ma‘abuta alherin suke ne?Ina malamai? Ina manyan mutane suke?  Ina muminai suke ne game da abubuwan sabani da ke aukuwa a tsakanin al‘umma?

Al‘amarin ya kai ga yin amfani da masallatai da Husainiyoyi da kuma tsoma bakin hukuma a sabanin masu addini, domin sabanin abu ne da hukumar take so,har ma ta kai ga wasu daga cikin ,‘ya‘yan wannan al‘ummar su ne suke kai wa hukuma rahoto game da abinda masu hidima wa addini suke gudanarwa, wannan kuwa duk sakamakon sabanin da ke aukuwa ne ta fuskoki dabam-daban.

Mu wai ba muna bukatar mu jawo wasu mutane masu daraja ba ne ko kuma fitattun malamai domin su zamo mana jigo illa iyaka su zamanto masu sasanta tsakani da hado kan jama‘a su dinke tsakani da kubutar da mu daga dariyar maqiya, yin haka na daga cikin manyan al‘amura.Manzon Allah (S) ya ce:-

“Shin ba na baku labarin abinda ya fi darajar salla da darajar azumi ba?.Shi ne sasanta tsakani ,domin bata tsakani shi ne mai halakarwa.“(Mizanul Hikma Juzu‘ii na 5 shafi na 362)

Allah Ta‘ala Ya ce:-

"انما المؤمنون اخوة فأ صلحوابين أخويكم".

(الحجرات/10)

“Muminai dai ‘yan‘uwan juna ne don haka ku sasanta tsakanin,’yan’uwanku“.

واصلحواذات واتقواالله.

(الأنفال:1)

“Ku ji tsoron Allah ku sasanta abinda yake tsakaninku’’.

Imam Ja‘afarus Sadiq (A.S.) ga wani Sahabinsa da ake kira Mufaddhal

ا

"اذا رأيت منازعة بين اثنين من شيعتنا فافتدها من مالي"

(الحكمةج ميزان5/363)

“Idan ka ga a tsakanin Shi‘awanmu guda biyu wata gardama to ka sulhunta daga dukiyata“.(Mizanul Hikma Juzu‘ii na 5 shafi na 363)

Imam Sadiq(A.S.) bai yarda da rashin jituwa a tsakanin mabiyansa guda biyu ne kawai ya yi wasiyya da a warware sabanin koda kuwa za a yi amfani da haqqinsa na dukiya.

To yaya Imam zai ji game da irin halin zamantakewar da ake ciki yau? Idan ya ga sabani da rikici a tsakanin Malamai da masu hudubobi da masu addini da sunan Shi‘anci da sunan Ahlul Bayt (A.S.) da sunan Marja‘i?

Watan Ramadhan dama ce mafi dacewa ta qoqarin kawo gyra a tsakani, da tabbatar da wasiyyar Imam Amirul Muminin(A.S.)

Na Hudu:رابعا:هي الله الله في القرآن -

“Allah Allah game da Alqura‘ani , kada wani da ba ku ba ya riga ku yin aiki da shi“.

Imam Baqir (A.S.) ya ce:-

“Kome yana da bazara, bazarar Alqura‘ani shi ne watan Ramadhana”.

“Duk wanda ya karanta aya daga Alqura‘ani a watan Ramdhana yana da lada kamar wanda ya sauke a Alqura‘ani baki daya a wani wata da ba Ramadhana ba”.

Saboda haka ya kamata mu ayyana lokacin karatun Alqura‘ani cikin tsarin rana-rana ta yadda za mu sauke shi aqalla sau daya a watan Ramadhana, Imam Ridha (A.S.) maganarsa kamar wani sashe ne daga Alqura‘ani kuma ya kasance yana sauke shi a cikin kowane kwana uku kuma yana cewa idan da na so da na dinga saukewa a mafi qarancin lokaci da ya gaza kwana uku amma na kasance ba na wuce wata aya har sai na yi tunani a kanta kuma mene ne dalilin saukar da ita”.(Littafin A‘immatuna na Ali Muhammad Ali Dhakilu Juzu‘ii na 2 shafi na 86)

Akwai hadisai da dama dangane da falala da kuma fa‘idojin karatun Alqura‘ani za mu kawo kadan daga cikinsu kamar yadda ya zo daga Manzon Allah (S) yana cewa:-

“Haqiqa zukata suna yin tsatsa kamar yadda qarfe yake yin tsatsa,sai aka ce Ya Manzon Allah mene ne kankare ta? Ya ce: Karatun Alqura‘ani“(Mizanul Hikmah Juzu‘ii na 8 shafi na 81)

“Ka dimanci karatun Alqura‘ani domin karanta shi kaffara ce ga zunubbai kuma shamaki ne ga wuta kuma aminci ne daga azaba “.(Mizanul Hikma Juzu‘i na 8 shafi na 81)

Wannan duk dangane da karantawa ke nan amma akwai dangane da haddacewa; a cikin jama‘armu ’yan qalilan ne suka haddace yanki mai yawa daga Alqura‘ani , duk da cewa an tanadi cibiyoyin koyon hadda, tare da shirya gasar hadda da ayyana kyautuka masu tsoka amma duk da haka masu zaburowa su shiga gasar ’yan qalilan ne sosai’’.

Alhalikuwa kuwa su muminai magata da yawansu sun kasance suna haddace Alqura‘ani ne a watan Ramadhana,kowa da ra‘ayin kansa yake haddace mafi yawan abinda zai iya na ayoyin Alqura‘ani ,musamman ma juzu‘in qarshe domin gajerun surori ne,da bayyanannun ma‘anoninsu na farkarwa cikin sauqi, ya zo a hadisai da dama dangane da haddace ayoyin Alqura‘ani.Manzon Allah (S) ya ce:-

“Ranar Alqiyama za a ce wa makarancin Alqura‘ani karanta ka qara hawa sama,ka rera kamar yadda ka kasance kana rerawa a gidan duniya domin darajar gidanka shi ne matsayin qarshe na abinda kake karantawa’’.

Akwai wasu hadisan kuma daga Imam Sadiq (A.S.) inda yake sanar da irin hasarar mutumin da ya haddace wani abu daga Alqura‘ani sa‘annan kuma ya manta shi.Imam ya ce wannan kamar mutum ne da ya kasance tare da wani aboki nasa wanda ya dade tare da shi amma kuma daga bayan sun yi wata da watanni tare sai ya mance sunansa.

Imam Sadiq (A.S.) ya ce:-

“Wanda ya mance da wata surar Alqura‘ani to za a kawo masa ita a kamannin wata kyakkyawar halitta mai daraja daukakakkiya a cikin Aljanna,idan ya gan ta sai ya ce , wace ce ke? amma akwai ki da kyawu ina ma da ke tawa ce.Sai ta ce masa

a‘a ba ka san ni ba ne? Ai nice sura kaza da kaza idan ba domin ka mance ni ba to da na dago ka zuwa wannan gurin“(Mizanul Hikma Juzu‘i na 8 shafi na 74)

Bangare na uku kuwa game da Alqura‘ani shi ne yin tuntuntuni game da Alqura‘ani,babu amfani sosai mutum ya karanta Alqura‘ani kawai ba tare da sanin ma‘anarsa ya yi tuntuntuni a kai ba.Ya zo a hadisi daga Imam Ali (A.S.)cewa:-

“ Ku sani cewa babu alheri a karatun da babu yin tutuntuni a cikinsa.“

(Mizanul Hikma Juzu‘ii na 8 shafi na 88)

Bilhasali ma Allah Ta‘ala Ya saukar da Alqura‘ani ne domin yin tuntuntuni a kansa kafin kome:-

“Littafi ne da Muka saukar shi gare ka mai albarka domin su yi tuntuntuni game da ayoyinsa“.

(Surar Swad aya 26)

Wasu daga cikin Musulmai suna raya cewa tuntuntuni game da Alqura‘ani ba a yarda da shi ba sai dai ga ma‘abuta zurfin ilimi, suna dogaro da wasu ruwayoyi da suka yi hanin tafsirin Alqura‘ani da ra‘ayi,sai  dai kuma su iriin wadannan ruwayoyin ba su dace da hikima ba sam sam domin Allah Shi ne Mafi sani game da LittafinSa da kuma halittunSa kuma Ya umarce su da yin tuntuntuni game da ayoyinSa.Bilhasali ma Ya yi magana ne da kowane mutum na kowane zamani da kowace qasa a Alqura‘aninSa inda Yake cewa:-

‘‘Wannan bayani ne ga Mutane da wa‘azi ga masu taqawa“.

(Surar Ali Imran aya ta 138)

Tambaya a nan ita ce :-

Shin zai yiwu Allah Ya aiko wa mutane littafi gaba dayansu sa‘an nan Ya hana su fahimtarsa da yin tuntuntuni a kansa to mene ne bayanin ke nan?

Alqura‘ani yana magana ne da mutane baki daya kamar yadda za mu gani cewa;“Ya ku mutane“ ko kuma magana da muminai cewa „“Ya ku wadanda suka

yi imani“,duk wannan jan hankali ne don a yi sauraro a ji saqon da ke biye da wannan fadakarwar,su fahimci jawabin su gane saqon.Duk da wannan shin zai yiwu mu raya cewa bai dace a yi tutuntuni a kansa ba?

Ba zai taba dacewa ba a ce ruwayoyi su hana tuntuntuni alhali kuma Allah Ya yi umarni da cewa a yi, sai dai kawai mu ce ruwayoyi sun yi hani game da wani abu dabam ko kuma mu ce ruwayoyin sun bayyana iyakar yin tuntuntunin ne da bai halatta a qetara iyakarsa ba.(Littafin Buhuthun Fil Qur‘anil Karim Juzu‘i na 17 shafi na 18)

Akwai wata al‘ada mai kyau a watan Ramadhana wadda ta dace da Alqura‘ani ;wannan kuwa ita ce a yawancin gidaje jama‘a sukan taru bayan shan ruwa daya daga cikinsu yana karanta Alqura‘ani sauran kuma duk su yi shiru suna saurarensa.Kowane dare sukan karanta juzu‘i daya ko fiye da haka.

Muna kira ga mutanenmu su yi riqo da wannan al‘adar, abu mafi dacewa kuma shi ne wani mai qwarewa game da ilimin Alqura‘ani ya kasance tare da su ya dinga yin bayani game da ma‘anarsa.

Ya zo a hadisi daga Manzon Allah (S) cewa“-

“Babu wata jama‘a da ta taru a daki daga dakunan Allah suna karanta littafin Allah suna yin tuntuntuni a kansa a tsakaninsu, har sai natsuwa ta sauko gare su,rahama kuma ta lullube su Mala‘iku kuma sun kewaye su Allah kuma Ya ambata su a cikin wadanda suke gurinSa“.(Mizanul Hikmah Juzu‘i na 8 shafi na 75)

Imam Ali (A.S.)yana da wata huduba da a cikinta yake siffanta mutane masu taqawa akwai wani sashe a cikinta kamar haka:-

خامسا:

الله الله في اللأيتم

Na Biyar:

“Ku tuna Allah, ku tuna Allah game da marayu, kada ku zalunci haqqoqinsu, kada a tozarta musu su a gurin da kuke hallare“.

A nan ba wai muna nufin yin bayani ne game da irin yadda maraya yake ji a cikin zuciyarsa ba ne sai dai kawai muna nufin yin ishara ne game da bukatar kulawa da shi a cikin al'umma saboda fa'idar yin haka a duniya da Lahira baki daya.

Domin shi maraya idan bai sami kulawa ba yana iya rikidewa ya zamanto wani qasurgumin dan ta'adda a sakamakon rashin samun tarbiyya da kuma rashin samun tausasawa alhali kuwa idan ya sami kulawa to da sannu zai kasance lafiyayye.

Akwai hadisai da dama da aka ruwaito inda suke yin nasihar himmatuwa game da marayu.

Ya zo daga Imam Ali (A.S.):-

"Babu wani mumini namiji ko mumina mace da zai sa hannu a kan kayin maraya har sai Allah Ya rubuta masa kyakkyawan aiki a kan duk wani gashi da hannunsa ya shafa.''(Mizanul Hikma Juzu'i na 1 shafi na 765)

Ya zo daga Manzon Allah (S) cewa:-

"Akwai wani Daki a Aljanna da ake kira "Dakin Farin Ciki'' wanda babu mai shigar sa sai wanda ya faranta wa marayan muminai rai".

(Mizanul Hikma Juzu'i na 1 shafi na 765)

Saboda haka babu makawa kiyayewa da kulawa da maraya musamman ma marayan da mahaifinsa ya mutu a tafarkin Allah.

A yau al'ummarmu cike take da marayu wadanda iyayensu suka bar duniya a tafarkin musulunci,nawa ne a Afghanistan?, nawa ne a Lebanon?nawa ne a sauran Qasashe? Haqiqa duk wadannan iyayensu sun yi shahada ne a tafarkin Allah saboda haka su amana ne a wuyan dukkanin al'ummar musulmi baki daya.

Wannan al'amari ne na musulunci da al'ummar musulmi,don dukkan wani maraya daga 'ya'yan shahidai su 'ya'ya ne na Musulunci kuma suna da haqqi mai girma a kan al'ummar Musulmi baki daya.Duk wanda aka kashe shi ya yi shahada a Iraqi ko a wata qasa ta Musulunci tunda ya yi shahada ne a wajen kare addinin

Musulunci a kowane guri yake ba wai kawai na wata qasa kebabbiya ta musamman ba.

Haqiqa nauyin marayun shahidai ya doru ne a kan kowa da kowa daga cikin Musulmi a duk inda yake.

Wannan wata na Ramdhana wata ne da lada yake qaruwa saboda haka ya dace kowa ya isar da tallafinsa da gudummawarsa ga ’ya’yan shahidai sawa‘un a nan qasar suke ko kuma a wata qasa.

Bayan ’ya’yan shahidai akwai wasu masu kama da ’ya’yan shahidai wadanda su ma suna bukatar taimakawa, wadannan su ne wadanda aka kama iyayensu.

A qasarmu akwai muminai da dama suna maqare a gidan kurkuku mai tsananin ban tsoro a bisa zargin cewa su masu tsaurin ra‘ayin addini ne, wasu daga cikinsu an yanke musu hukuncin daurin rai da rai ko kuma na tsawon shekaru masu yawa wanda ke nufin cewa an haramta wa ’ya’yansu tausasawa da jin dadin zama da su, da kewar zamantakewar iyali saboda haka su ma dai kamar ’ya’yan shahidai amana ce a wuyan kowa da kowa.

Watan Ramadana dama ce mai kyau ta kai ziyara ga iyalansu da tausasa musu da kyautata musu.

Abu da ake bukata ba wai kawai taimakon abin duniya ba ne har ma da tausasawa da tausayawa irin na ’yan Adamtaka, da yin magana da su ta waya ko rubuta musu saqo, ko kai musu ziyara a duk inda suke da ba su kyaututtuka, duk wannan zai qarfafa musu gwiwa ya faranta musu zuciya sosai.

الله الله في الجهاد

Na Shida:

“Ku tuna Allah ku tuna Allah dangane da Jihadi a tafarkin Allah da dukiyarku da rayukanku da harsunanku.“

“Haqiqa Jihadi shi ne mafificin ayyuka bayan Musulunci. Shi ne madogara ga Musulunci, ladansa kuma yana da yawa,da daukaka,da ni‘ima ,shi maimayi ne ga

kyawawan al‘amura,kuma albishirin Aljanna bayan shahada.“(Mizanul Hikmah Littafi na2 shafi na 125)

Duk da muhimmancinsa’yan qalilan ne daga cikin al‘umma suke yinsa saboda jahilci,da tsoro,da fargaba, da koma baya,sai dai kawai jama‘ar Iraniyawa wadanda Allah Ya yi musa ni‘ima ta yadda har suke sanar da fita zuwa jihadi kuma suna kwadayinsa;duk yayin da aka yi kira ko sanarwar fita zuwa jihadi nan da nan za ka ga daruruwan dubbai sun fito ,haka nan a Lebanon haka nan a Afghanistan,alhali sauran qasashenmu batun yin jihadi har yanzu tukuna baqon abu ne,kamar yadda su jama‘ar masu jihadin kansu ba sa rabuwa da ’yan sukan ra’ayi game da su domin ana kiran su masu ra‘ayin mazan jiya da kuma masu zafin ra’ayi.

Imam Ali (A.S.) a wasiyyarsa ta qarshe a watan Ramadhan, kamar yadda ya gabata ya qulla tsakanin Jihadi da Azumi inda ya ce :-“Zakkar jiki Jihadi ne da Azumi“.

A wasiyyar tasa ya yi maganar jihadi iri uku :-

Jihadi da dukiya

Domin shan gaban makeken kasafin kudin gwamnatoci ke fitarwa don qarfafa ma‘aikatunsu da ayyukansu,domin fuskantar dimbim dukiyar da maqiyan musulunci suke bayarwa don makircinsu da fito na foto da al‘ummarmu, ba zai taba yiwuwa ba ga masu aiki wa addini a tafarkin Allah, su iya ci gaba da gwagwarmaya in ba a qarfafa su daga al‘umma da mawadatan cikin al‘ummar ba.

Babu shakka a qasashenmu akwai mawadata da yawa, attajirai da ’yan kasuwa sai dai abin baqin ciki shi ne cewa suna tsuke bakin aljihunsu, ba sa bayar da gudummawa wajen yin ayyuka a tafarkin Allah, idan har wani daga cikinsu ya zaburo wajen fitarwa a tafarkin Allah sai ya qare a ayyukan da aka saba da su a cikin al‘umma wato kamar su gina masallaci da taimakon gajiyayyu.Amma wajen fitarwa don yin jihadi a tafarkin Allah,da gwabzawa da maqiyan Musulunci wannan abu ne da babu wani daga cikin mawadatanmu da yake  tunaninsa a qasashenmu.

Kuma su mawadatan ba wai sun jahilci samuwar masu jihadi a tafarkin Allah ba ne illa iyaka dai kawai sun gafala ne ko kuma sun gafalar da kansu ne game da abinda ya wajaba a kansu dangane da jihadi a tafarkin Allah.

Kaiton masu dukiya ina ma da sun fadaka sun yi tunani game da rayuwarsu ta gaba,da dukiyarsu da irin hatsarin da ke fuskanto su nan gaba idan har ba su tashi sun sha gaban maqiya da azzalumai ba.

Muna da darasi daga abin da ya faru a Iraqi inda masu arziki muminai suka qi taimaka wa masu gwawarmayar addinin Musulunci suka bari Miyagun 'Yan Jam'iyyar Ba'athawa suka yi kaka gida a kan mulkin inda a qarshe kuma ba su bar wata alfarma ta addini ko ta jini ko ta dukiya ta tsira ba.

Dubban Muminan da Ba'athawa suka qwace musu dukiyarsu a Iraq , suka tilasta su zuwa gudun hijira, duk suna nadama a yau,nadamar da ba za ta yi musu amfani ba saboda sakacin da suka yi na qin taimakawa musulmai masu gwagwarmaya.

Sauran shugabannin qasashen musulmi ba su gaza Saddam da Jam'iyyarsa ta Ba'athawa Azzaluma a kaushin zuciya ba.Amirul Muminina(A.S.) ya yi gaskiya inda a wani sashen na wannan wasiyyar ya ce:-

"Kada ku dena yin umarni da kyakkyawan aiki da hana mummunan aiki, (domin in kun dena) sai Ya sanya ashararanku su zama shugabanninku sa'annan ku yi addu'a ba zai amsa muku ba."

(2)Jihadi sadaukar da rai

"Yaqi tsakanin Musulunci da Kafirci na gudana a halin yanzu, kafirai suna tanadin duk abinda za su iya na qarfi da qwarewarsu domin tabbatar da kaka gidansu a kan al'ummarmu musulunci; to matuqar Muminai ba su tokare wannan mugun hari na kafirai ba da sannu Kafiran za su tumbuke duk wani sauran jigo na Musulunci da ya saura a qasashen Musulmi daga asasinsa kuma za mu zama cikin karyewa da baqin ciki da ci baya.

Fuskantar harin maqiya yana bukatar shiryawa ga’ya’yan wannan al‘umma game da sadaukar da rai saboda Allah....kamar yadda ’yan’uwanmu suke yi a Afghanistan da Iran da Lebanon...

Masu qarfi daga cikin wannan al‘umma tamu su yi gaggawa domin shigewa cikin tawagar Juyin Juya hali da Jihadi su qudiri aniyar zage damtse a kan aiki saboda Allah.Babu mafi dadin salon zaburarwa da kwadaitarwa zuwa Jihadi da sadaukarwa saboda  Allah ya zo kamar haka:-

Jihadi da harshe

Jihadin harshe shi ne jihadi ta hanyar yada ra‘ayin kawo juyi ,ta hanyar kiran mutane zuwa ga Jihadi da kare masu jihadi a tafarkin Allah.

Duk wani mai kishi to ya kare masu aiki a bisa tafarkin Allah domin hukuma da masu ra‘ayin mazan jiya suna yada munanan tuhumce-tuhumce game da su domin hana mutane zuwa kusa da su ko yarda su.

Mujahidai ba yaqi suke yi don kare kansu ba ko kuma don kare fa‘idar kansu sai dai kawai suna jure cutarwa da wahalhalu ne saboda addini da darajar al‘umma,saboda haka bai dace ba ga wani mumini ya zamanto yana da hannu wajen bata su, ba ma wannan ba bai halatta ba a yi shuru game da qoqarin maqiya na bata musu suna. Manzon Allah(S) ya ce:-

“Wanda ya yi ghibar mai yaqi ko kuma ya cutar da shi ko kuma ya munana wakilcinsa a iyalansa da ya bari a baya za a kafa masa tuta Ranar Al-Qiyama kuma a gama da duk kyawawan aikinsa sa‘annan a jefa shi a wutar Jahannama.“(Mizanul Hikma Juzu‘i na 2 shafi na 128)

Na bakwai:

Kada ku kashe kowa sai wanda ya kashe ni

‘‘ Ya ku Banu Abdulmuttalib kada in same ku kun kwararar da jinin musulmai malala kuna da’awar cewa an kashe Amirul Muminina.

“Ku ji ku sani kada ku kashe kowa saboda ni sai dai wanda ya kashe ni kawai. Ku jira idan har na mutu a sakamakon saran da ya yi mini to ku yi masa saran kwaf daya kuma kada ku yi gunduwa da shi;domin na ji Manzon Allah (S) yana cewa: “Ku kiyayi kanku kada ku yin gunduwa gunduwa da gawa ko da kuwa gawar mahaukacin kare ne“.

Wannan ma‘ana mai girman da daraja na jawo hankalinmu zuwa ga halin da siyasar al‘ummarmu ta musulunci take ciki da kuma yadda ya kamata ta kasance.

Imam Ali (A.S.) duk da girman matsayin da yake da shi a gurin Allah ya qi amincewa a zubar da jini saboda shi ko kuma saboda ransa shi kadai,alhali a yau muna rayuwa a qarqashin shugabanni masu kiran kansu “Masu, masu martaba“ wadanda alal haqiqa ba su cancanci wannan siffantawar ba ko da gwargwadon harafi daya.Kwanakin da suka wuce aka hukunta wasu muminai a daya daga cikin qasashen wannan yankin da zargin cewa wai sun muzanta sunan daya daga cikin dayan shugabannin da ke kiran kansa ,‘‘Mai girma,mai daraja’’.

Alal haqiqa shugaba adali shi ne shugaban da ba ya amfani da qarfi wajen murqushe jama‘arsa ko keta haddinsu,kuma ba ya ba wa kansa ko iyalansa haqqi fiye da sauran jama‘a,ko kuma ya kewaye kansa da bambadawa da ke kambama shi da tsarkake shi ta yadda cin gyaransa ko sukan ra‘ayinsa kawai ya zamanto laifin da ba za a taba yafewa ba ko kuma a kai duk wanda ya yi haka gidan yari.

Yayin da Imam Ali(A.S.) yake fadin wannan magana tasa game da wanda ya kashe shi to ya zamanto darasi da wa‘azi mai girma.Kai hatta kafin wannan ma ya kasance ya saukar da kansa ga daraja irin ta kowane talaka yana rayuwa kamar sauran mutane duk da cewa shi ne shugaba khalifa.

Akwai qissosi game da adalcinsa da qan-qan da kansa da dama wadanda tarihi ya kawo mana.

“An ruwaito cewa wata rana Imam Ali (A.S.) yana zaune a tare da jama‘a a garin Kufa sai wata mata ta zo ta wuce kusa da su sai maza suka quqqura mata ido sai Imam (A.S.) ya tsawatar musu game da haka ya ce:

“Idandunan wadannan mutane masu kwadayi ne, wannan kuma na iya kai su ga halaka ,duk wanda ya ji sha‘awar wata mata to ya shafi matarsa domin ita ma mace ce kamar kowace mace.“ Sai wani daga cikin Khawarijawa ya ce :“Allah Ya halaka shi kafirin masani“,sai jama‘a suka zaburo masa za su ladabtar da shi,sai Imam (A.S.) ya dakatar da su yana cewa: “Sai dai ramuwar zagi da zagi ko yin afuwa ga laifi,daga nan sai ya yi masa afuwa ya qyale shi.“(Littafin As-Sabil ila inqaadhil Muslimin shafi na 440)

A wata ruwayar kuma ya kasance yana sallar Asuba sai wani daga cikin munafukai mai suna Ibin Kuwaa ya karanto ayar Alqura‘ani da ke cewa:

“Kuma haqiqa Mun yi wahayi gare ka da kuma zuwa ga wadanda suke kafin kai cewa lalle idan har ka yi shirka to haqiqa aikinka zai baci kuma za ka kasance daga cikin wadanda suka yi hasara.“

Ya yi haka ne kawai don qalubalantar Imam domin a ra‘ayinsu Imam ya yi shirka tunda ya yarda da sulhu, sai Imam (A.S.)ya dakata karatu don aya na cewa: “Idan ana karatun Alqura‘ani ku saurara ku yi shiru“ .Da Ibin Kuwaa ya yi shiru sai Imam ya ci gaba da karatu daga nan sai Ibin Kuwaa ya sake fara karatu a karo na biyu har karo na uku.Da ya yi na uku sai Imam (A.S.)ya karanto wannnan ayar da ke cewa:-

“Ka yi haquri haqiqa wa‘adin Allah gaskiya ne ,kada wadanda ba su da yaqini su wofantar da kai“.

Domin mu fahinci darajar Imam da qanqan da kansa muna iya yin tambaya kamar haka:-

‘‘Me zai auku idan abinda aka yi wa Imam ga wani daga cikin shugabannin yankin nan,ko kuma a ce wani ya zo gabansa ya rubuta masa wannan ayar da ke cewa:-

“Haqiqa Sarakuna idan suka shiga gari suna bata shi ,kuma suna sanya madaukakansu su zamanto maqasqanta,haka nan suke aikatawa.’’

Tarihi ya kawo mana yadda daya daga cikin Khalifofi ya kasance yana fusata a sakamakon yadda wani daga cikin manyan sahabbai Abu Zarril Ghifari yake yawan karanta ayar da ke cewa:-

“Kuma wadanda suke taskance zinare da azurfa ba sa ciyar da su a tafarkin Allah to ku ba su albishir da azaba mai radadi“.(Surar Tawbah aya ta 34-35)  Saboda ya dauki karanto wannan ayar tamkar suka ne gare shi,da siyasarsa da tsarin tattalin arzikinsa sai ya kori Abu Zar zuwa gudun hijira a Rabdah inda ya mutu shi kadai tal a gurin ba kowa.

Ibin Abi Hadid yana cewa: “Ka sani cewa abinda mafi yawan malaman tarihin musulunci da na hadisi  suka tafi a kai shi ne cewa da farko Usman ya kori Abu Zar zuwa Sham,daga nan ya dawo da shi Madina yayin da Mu‘awiya ya kai qarar sa, daga nan kuma ya kore shi daga Madina zuwa Rabdah saboda a Madina ya ci gaba da yin abinda ya kasance yana yi a Sham“

Asalin wannan al‘amari shi ne yayin da Usman ya ba wa Marwan bin Hakam da wasunsa gidaje da dukiyoyi , kuma ya kebe wata ga Zaid bin Thabit;sai shi Abu Zar ya dinga fita kwararo da hanyoyi a Madina yana cewa:

“Ka yi albishir ga kafirai da azaba mai radadi“  yana daga murya yana karanto ayar Allah Ta‘ala cewa:-

".أليم بعذاب فبشرهم الله سبيل في والفضةولاينفقونها الذهب يكنزون والذين"

"والذين يكنزون الذهب والفضة و لا ينفقونها في سبيل الله فبشر هم بعذاب أليم"

(التوبة:34-35)

“Wadanda suke taskance zinare da azurfa ba sa ciyar da su a tafarkin Allah ka yi musu albishir da azaba mai radadi.“Sai aka kai labarin haka ga  Usman a kai a kai amma amma ya yi shiru.

Daga bisani sai Usman ya aiki wani daga cikin masu hidimarsa zuwa gurin Abu Zar cewa: “Ka dena abinda ya iso gare ni cewa kana aikatawa“. Sai Abu Zar ya amsa masa da cewa:-

“Ko kuma Usman ya hana ni karanta littafin Allah ba, aibu ne a bar karanta Alqura‘ani,na rantse da Allah samun yardar da Allah ta hanyar fusatar da Usman ya fi mini alheri fiye da samun fushin Allah saboda yardar Usman“.(Sharhin Nahjul Balagha shafi na 251-252)

Haqiqa a yau muna da matuqar bukatar tafarkin Amirul Muminina Aliyu bin Abi Talib (A.S.) a siyasa da zamantakewa domin mu gane irin fandarewar da shugabanni suka yi da sunan Musulunci,sa‘an nan haqiqanin surar rayuwar zamantakewa ta bayyana gare mu a rayuwar Imaminmu, yaya shugaba ya kamata ya zama, yaya zai rayu da mutanensa.

Ibin Athir ya ruwaito a littafin tarihinsa “Al-Kamil“,cewa “Ali bin Abi Talib“ ya sami garkuwarsa a gurin wani Kirista sai ya kai shi qara gurin Alqalinsa Shurayhi,aka zauna shari‘a Imam Ali (A.S.) ya ce wannan garkuwa ta ce ban bayar da ita kyauta ba, kuma ban sayar da ita ba .Sai Alqali Shurayh ya ce wa Kiristan me za ka ce game da abinda Amirul Muminina ya ce? Sai Kiristan ya ce: Garkuwa garkuwa ta ce Amirul Muminina kuma bai yi qarya ba.Sai Shurayh ya juya kan Imam(A.S.) ya ce masa „“Ya Amirul Mumina ko kana da wata shaida?

Daga bisani sai Amirul Muminina ya murmushi ya ce: “Ba ni da shaida.“ A sakamakon haka sai Alqali Shurayh ya yanke hukunci ya ba wa Kirista garkuwa.Banasare ya dauki garkuwa ya yi tafiyarsa Amirul Muminina yana kallon sa.

Banasare na cikin tafiya bai yi nisa ba sai ya dawo yana cewa:-

“Ni ina ba da shaidar cewa wannan hukuncin Annabawa ne, Amirul Muminina ya kai ni gurin Alqalinsa, Alqalin nasa kuma ya ba shi rashin gaskiya : haqiqanin al‘amarin shi ne cewa wallahi garkuwa ta Amirul Muminina ce .’’

Malaman tarihi sun ruwaito cewa yayin da Imam ya yi nasara a kan Khawarijawa su kuma suka ci gaba da sukan martabarsa suna kafirta shi suna kirarin cewa"Babu hukunci sai na Allah,wanda kalma ce ta gaskiya da aka nufi qarya da ita,kamar yadda shi Imam(A.S.) ya fada da kansa. Imam(A.S.) bai musu raddi da mummunan raddi ba, bilhasali ya kasance yana ba su kasafi daga Baitulmali.

Sahabban Imam Ali(A.S.) sun so a yaqe su amma Imam (A.S.) ya qi amince musu kuma ya hana yin haka a sarari ya ce:-

"Idan suka yi shiru za mu qyale su,idan suka yi magana za mu qure musu hujja idan suka yi fasadi za mu yaqe su".(Littafin Sabilun Ila inqaadhil Muslimin shafi na 452)

Haka nan Imam Ali (A.S.) ya aiwatar da musulunci a aikace ya ba wa musulmai kyakkyawan misalin shugaba adali na addinin musulunci wanda bai ba wa kansa wasu kebantattun haqqoqi na musamman ba kuma bai kewaye kansa da kantagar da'awar wata tsarkaka ba kuma bai hana mutane haqqin bayyana ra'ayinsu ba ko bayyana hamayyarsu.

A wasiyyarsa ta qarshe akwai abin dubawa da yin tuntuntuni domin koyar darrusa dangane da gaskiya da adalci.

Da fatan Allah Ya lullube mu a rahamarSa mayalwaciya, a wannan wata mai girma.

.